ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org)
Is A Capacity Building Civil Society Organization
Whose Activities Covers Research, Advocacy,
Training And Publicity In All Areas Of Icts.
Its Vision Is; A Knowledge-based Democratic Society
Free Of Hunger While Its
Mission Is; Using ICTs To Empower Citizens For
A Just And Knowledge-based Society
That Is Anchored On Sustainable
And Balanced Development.

MAIN OFFICE:
3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social
Insurance Road, Behind Trade Fair Complex,
Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467 •
E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org,
Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

BAUCHI OFFICE:
NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House,
Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312

CITAD.....*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

Tsarawar
Cibiyar Bunkasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar kungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)

KUNDIN SAMAR DA CIGABAN GARIN 'YAMMEDI

CITAD

CENTRE FOR INFORMATION TECHNOLOGY AND DEVELOPMENT

KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN GARIN 'YAMMEDI

Tsarawar

Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)
Tare Da
Gudummawar Kungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)

ABUBUWAN DA KE CIKI

Shafin Farko.....i
Jadawali.....ii
Godiya.....1
Gabatarwa.....2
Manufa.....3
Hanyoyin Da Aka Yi Amfani Da Su.....3
Tsarin Da Aka Yi Amfani Da Shi.....3/4
Cikakken Bayani Game Da Garin Daura.....4/6
Kadarori.....7
Jujjuyawar Yanayi.....7
Tarihin Garin Daura.....8
Taswirar Garin Daura.....9
Yanayin Zamantakewa.....10
Lafiya.....11
Ilimi.....12/13
Juyawar Yanayin.....14
Jadawalin Juyawar Yanayi na tsahon Shekara.....14/15
Kadarori.....15
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Garin.....16
Tantance Haƙƙoƙin Mata.....17/18
Jadawali Ayyukan Yau Da Kullun.....19
Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam.....20/21
Kalubalen Da Ke Fuskantar Garin 'Yammedi A Halin Yanzu.....22/24
Sassaukar Hanyar Jera Matsaloli.....24/26
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli.....27/28
Jadawalin Tantance Matsaloli Garin 'Yammedi.....28/29
Tantance Yanayin Karfin Iko (Nazari Kan Waɗanda Keda Iko).....30/31
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai.....31/32
Tsarin Da Aka Shirya Gudanarwa Na Al`Umar Garin 'Yammedi.....33/34

GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na 'Yammedi da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.

GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan gari yana ɗauke da taƙaitattun bayanai game da garin 'Yammedi. An tattaro waɗannan bayanai ne ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya da kuma sabon tsarin nan na CITAD/ActionAid wanda ke bai wa kowa damar bayar da gudummawarsa. Wannan tsarin ginshiƙi ne na aikin CITAD/ActionAid da al'umma a mataki na gaba. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya. Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike game da mutanen da ke rayuwa cikin talauci ta ɗaya daga cikin waɗanan hanyoyin:Binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa garin barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama,CITAD ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a garin 'Yammedi cikin Karamar Hukumar Karaye ta Jihar Kano. Bayanan da aka tattara a ƙarƙashin wannan tsarin za suyi amfani domin zama ginshiƙai na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gabatar da bayanai game da garin 'Yammediwanda zasu taimaka wajen ragewa jama'a raɗaɗin talauci da abubuwan da ke yiwa ɗaiɗaikun al'ummar garin tarnaƙidama iyalai gabakiɗaya ya kuma samar da cigaban garin.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da garin 'Yammedi ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

MANUFOFIN TSARIN WAIWAYE ADON TAFIYA

- Tattara bayanan sakamakon da aka samu dangani da manufofin shirin CITAD/Actionaid
- Tattara sahihan bayanan garin 'Yammedi wanɗanda zasu iya zama sanadiyar cigaban garin.

HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen garina tsawon kwanaki 3 domin samun cikakkun bayanai na ɓangarorin nan bakwai na Reflection Action.
- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan garin 'Yammedi da CITAD.
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori nanbakwai na waiwaye adon tafiya wato Reflection Action.

An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabar garin.

An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙi ɗan Adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar garin 'Yammedi.

Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.

An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.

An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iyabayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.

An yi amfani da tsarin zane naVenn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.

An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.

Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.

Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garin ke isar da saƙonni tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

Cikakken Bayani Game Da Garin 'Yammedi

Sunan Garin:	'Yammedi
Karamar Hukuma:	Karaye
Jiha:	Kano
Adadin Al'umma:	23,275 (Maza: 12,644, Mata: 10,631)
Adadin Magidantan Garin:	17,881
Adadin Dattijai Magidanta:	1,819
Adadin Mata Magidanta:	636
Adadin Yara Magidanta:	18

AJUJUWAN SHEKARU	KIYASI
Shekara 0 zuwa 5:	4,586
Shekara 6 zuwa 10:	4,260
Shekara 11 zuwa 18:	5,182
Shekara 19 zuwa 30:	8,130
Shekara 31 zuwa 40:	4,871
Shekara 41 zuwa 50:	7,180
Shekara 51 zuwa 60:	5,452
Shekara 61 zuwa 70:	1,387
Shekara 70 zuwa sama:	338
Adadin Al'ummar Gabaɗaya:=	

Madogara: ɗaya daga cikin mahalarta taron samar da kundin cigaban garin

SANA'OI/AIKIN YI: Noma (Noman Hatsi), Kiwon Shanu, Kasuwanci (Yan tireda) da Ma'aikatan Gwamnati.

KAYAYYAKIN ABINCIN DA AKE NOMAWA A GARIN: Gero, Dawa, Wake, Masara, Gyaɗa da Kayan Miya.

KUƊAƊEN DA KE SHIGOWA/KUƊAƊEN DA AKE KASHEWA

Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: **N 200,000**

Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara: **N200,000**

Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a shekara: **N450,000**

Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara: **N450,000**

KUƊAƊEN DA KE SHIGOWA

Adadin Mutanen da suka mallaki gonaki da ƙananan sana'o'i: Kowanne magidanci kan mallaki gonaki.

Adadin matan da suka mallaki gonaki da ƙananan sana'o'i: Ɗaukacin matan garin kan shiga a dama dasu wajen ɗaya daga cikin sana'o'in dake akwai a garin. Yawancinsu kanyi kiwon dabbobi kamar awaki, tumaki da kaji.Haka kuma ƙalilan daga cikinsu sun mallaki shanu.

LAFIYA				
Cin Moriyar Ɗakunan Shan Magani	Gwargwadon nisan ɗakin shan magani da al'umma kilomita 5 zuwa 6			
Wadatattun Kwararrun ma'aikatan lafiya	Idan haka ne ayi tik	Idan haka ne, su nawa ne? Gaɓaɗaya : 12 Maza: 8 Mata: 4	Ana samun ma'aikatan kodayaushe?	Ana samunsu kodayaushe.
Yaya ake warware matsalar annoba?	Ana warware matsalar annoba ta hanyar kulawa da marasa lafiya da keɓance su daga cikin mutane da kuma basu shawarwari.			
A ina ake karɓar haihuwa?	Kalilan daga cikin matan garin kan haihu a ɗakunan shan magani garin.			
Yaya ake magance haihuwar da tazo da matsala.	A kan tura su babban asibitin garin Gwarzo			
An sami cigaba a harkokin lafiya a wannan gari shekaru 3 da suka wuce?	Har yanzu babu wani cigaba da ake samu a harkokin lafiya a wannan gari.			

ILIMI

Makarantu: Makarantar Firamare guda ɗayace a Garin.

Adadin yaran da suka shiga makaranta a halin yanzu: 1,400	Adadin yara maza: 1033	Adadin yara mata: 367	Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: 43
	Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: 71	Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: 56	Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20: (idan ana buƙata)
Adadin waɗanda suka kammala firamare a garin:146			Adadin Maza: 88 Adadin Mata: 58
Adadin waɗanda suka kammala sakandare a garin: 220			Adadin Maza: 135 Adadin Mata: 85
Adadin waɗanda suka kammala makarantar gaba da sakandare a garin: 120			Adadin Maza: 69 Adadin Mata: 51
Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa makaranta ba: 62			Adadin Maza: 17 Adadin Mata: 45

KADARORI

Adadin matan da suka mallaki filaye/gonaki: babu wani takamemen ƙiyasin matan da suka mallaki filaye ko gonaki, sai dai jama'ar garin sun bayyana cewa mata na da cikakken ikon mallakar kadarori a garin. Da yawa daga cikin matan sun mallaki gonaki da dabbobi.

JUJJUYAWAR YANAYI

Samun ruwan sama ya kai mizanin 42.8 digiri a ma'aunin samun ruwan sama	Lukutan samun ruwan sama (watanni) Watanni 6	Tsahon lokacin samun ruwan sama (a watanni) wata 6	Wajen da ake samun ruwa mafi kusa (ƙasa da rabin kilomita kwatan--kwacin tafiyara ƙasa da minti 5
Kadarori (ƙiyasi)	Kiyasin adadin waɗanda suka mallaki gonaki da ƙananan yan kasuwa **15,631**	Adadin mazan da suka mallaki gonaki da ƙananan yan kasuwa maza **11,330**	Adadin matan da suka mallaki gonaki da ƙananan yan kasuwa mata **4,301**
Masu buƙata ta musamman	Adadin yawan masu buƙata ta musamman: 23(ƙiyasi)	Adadin maza masu buƙata ta musamman: 15(ƙiyasi)	Adadin mata masu buƙata ta musamman: 15 (ƙiyasi)

TARIHIN GARIN 'YAMMEDI

Garin 'Yammedi ɗaya ne daga cikin garuruwan da ke ƙaramar hukumar Karaye, an ciro garin ne daga cikin garin Dafka a shekarar 1922. Garin 'Yammedi ya tattara ƙananan ƙyauka 9 waɗanda suka haɗada 'Yammedi Cikin Gari, Unguwar Maƙera, Unguwar Taiki, Albishirawa, Jama'ar Kison, Unguwar Kure, Audawa da Tsohuwar Karaye. Babajo shi ne sunan sarkin garin na farko, sai Amadu Kwano, sai Muhammad Abdu, sai Ahulu Abdulƙadir, sai Garba Sarkin Kafi sai Adamu sannan Abdulƙadir Aliyu. Garin 'Yammedi na maƙwotaka da garin Dederi daga arewa, yana maƙwotaka da garin Kafin-Dafga da kudu, daga gabas kuma yana maƙwotaka da garin Madobawa da garin Kuragu da kuma garin Kumbugawa, daga yammacin garin kuma kogi ne. A ƙiyasance garin na adadin al'ummar da yakai kusan 24,000.

Garin nada ɗakin shan magani guda ɗaya dake cikin garin sai kuma wani ƙaramin ɗakin kula da lafiyar dake unguwar Kure. Makaratun firamare biyu ke akwai a garin, ɗaya na cikin garin ɗaya kuma na Taiki sai makarantar islamiyya a Kangarwa da Audawa da Unguwar Kure da kuma Maƙera.

Ayyukan noma su aka fi yawan yi a garin (noma da kiwo), Allah ya albarkacin garin da masu ilimin boko da ilimin addini. Haka kuma akwai sanannun yan siyasa a garin (shi kansa ɗan majalisar jiha dake wakiltar ƙaramar hukumar Karaye ɗan garin 'Yammedin ne.)

Yanayin da ilim ke ciki a garin ya zama abin kwatance idan akayi la'akari da ƙarancin ajujuwa da na malamai da makarata ƙwalli ɗaya da garin ke da ita, lamarin da ke mutuƙar shafar zuwan yara makaranta. Rashin aikinyi yayi mutuƙar yiwa garin katutu ga ƙarancin sana'o'i da mata da masu buƙata ta musamman ke fama da shi.

'Yammedi gari ne na manoma wanda ake ayyukan noma cikinsa a tsahon shekara. Kodayake, idan rani yayi tsaho manoman garin kan haɗu da yan matsaloli yadda amfani gona bai samun ishashshen ruwa musamman noman rani duk da hanyoyin samun ruwan da suka haɗa da na rijiyoyi da kogi da garin ke dashi. Noman ranin da akeyi a garin zai ɗauki tsahon lokaci kafin ya cimma matsalolin da garin ke fuskanta.Ɗakin shan maganin garin baya iya biyan buƙatun lafiyar jama'ar garin domin ƙarancin ma'aikata dana kayayyakin aiki. Sannan kuma ga ƙarancin tsabtaceccen ruwan sha da garin ke fama dashi.

TASWIRAR GARIN 'YAMMEDI

Samar da taswirar ya soma ne da tattaki cikin ƙwaryar garin.Tattakin ya bayar da damar samun gamsassun bayani game da garin, matsaloli da damarmakin dake akwai a garin. Muhimman abubuwan da aka gano sun haɗa da ababan more rayuwa, albarkatun ƙasa. Taswirar ta nuna yadda garin yake a yanzu da kuma irin canje-canje da garin ke son cimmawa a gaba. Taswirar ta kuma nuna guraren da suka haɗa da gidaje, makaranta, masallaci, ɗakunan shan magani, kasuwa, rijiyoyi a duk inda suke a cikin garin



Yemmedi Community Map

Jama'ar Garin Ke Tattaunawa Lokacin Samar Da Tasawirar Garin

YANAYIN ZAMANTAKEWA

Garin 'Yammedigarine dake da yawan jama'ar da suka kai adadin ƙiyasi23,275 (Maza: 12,644, Mata: 10,631). Bugu da ƙari, mutanen wannan garin yawancinsu Manomane na hatsi da kiwo. Matsakaicin abin da ke shigowa mutum magidanci a shekarashi ne N200,000.Matsakaicin abin da ke shigowa mutum magidanci a kullum yakai N450.Haka kuma Matsakaicin abinda ke kashewa a shekara yakai N200,000, (matsakaicin abinda Mutum magidanci ke kashewa a kullum yakai N450.A wani gefen kuma, Matsakaicin abin da ma'aikaci ke samu a shekara shi ne N450,000 sannan kuma matsakaicin abin da ma'aikaci ke kashewa a shekara shi ne N450, 000

LAFIYA

Ɗakin shan magani guda ɗaya ake dashi a garin wanda gwamnati ta gina. Ɗakin shan magani na da ƙwararrun ma'aikata 5 daga cikinsu 3 maza ne sauran 2 kuma Mata.

Gudumowar da Ɗakin Shan Magani ke bayarwa ga jama'ar gari bata kai ta kawo ba. Mutanen wannan garin kanyi tafiyar misalin kilomita 5 - 6 zuwa hedikwatar ƙaramar hukumar garin domin samun ingantancciyar kulawa dangani da abin da ya shafi neman lafiyarsu. Hakan ba ƙaramar wahala ke jawowa marasa lafiyar ba musamman mata masu juna biyu. Haka kuma wannan na faruwa ne idan akayi duba da yanayin gurbacewar da titin garin ke fama dashi.

ILIMI

Akwai makarantar firamare guda ɗaya a cikin garin, makarantar na ɗauke da rukunin ginin ajujuwa guda huɗu, ɗaya daga cikin rukunin gini wadda gwamnati ta gina na ɗauke da ajujuwa guda 8 sannan sauran rukunin ginin na ɗauke da ajujuwa guda 4. Adadin yara 370 suka shiga makaranta a halin yanzu (197 maza 173 mata). Wannan shi ya nuna cewa adadin yara maza da suka shiga makaranta ya fi na yan uwansa mata. Dama iri ɗaya ake bawa mata wajen samun ilimi da yan uwansu maza. Hakan kuwa ya faru ne sakamakon irin gudunmowar da wasu dattijan garin ke bayarwa musamman mai unguwa wanda tsohon ma'aikaci ne a ma'akatar albarkatun ruwa. Bugu da ƙari, adadin mutum 146 ne suka kammala makarantar firamare a garin, yayinda adadin mutum 220 suka kammala makarantar sikandire a garin, haka kuma mutum 120 suka kammala makarantar gaba da sikandire. Sai dai cewa sama da mutum 92 (maza 47 mata 52) basu taɓa halartar makaranta ba. Wannan shi yake nuna cewa kafin wannan yunƙuri, a baya adadin matan da ake ɗauka a makaranta basu taka kara sun karya ba.

Anyi amfani da Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS domin tantance inganci ilimi a garin 'Yammedi.Shirin bunƙasa damar samun ilimi PRS ya fayyace haƙƙoƙi guda 10 da aka samu daga dokokin ƙasa misali anyi amfani da kundin tsarin mulkin ƙasa da tarukan kare haƙin ɗan adam wajen tantance ingancin ilimi a garin 'Yammedi.

Babbar manifar wannan shiri na PRS shine shigar da yan ƙasa cikin tsarin bunkasa ilimi. Anyi amfani da kundin wajen tantance mizanin fahimtar damar samun ilimi musamman ta fuskar al`umar wannan gari susan cewar damar suce.Tare da mizani mai lamba 1 mafi ƙaranci da lamba 5 mafi girma. Jadawalin da ke tafe yayi ƙarin haske

GA JEREN HAKKOKIN:

LAMBA	HAKKOKI (SHIRIN BUNKASA DAMAR SAMUN ILIMI PRS NA GARIN 'YAMMEDI)	TANTACEWA (1 MAFI KARANCI, 5 MAFI GIRMA)
1.	Haƙƙokin samun kyakkyawan ilimi kuma kyauta	3
2.	Haƙƙokin rashin nuna wariya	4
3.	Haƙƙokin samar da isassun kayayyakin more rayuwa	5
4.	Haƙƙokin samar da wajen zama mara haɗari	5
5.	Haƙƙokin samara da ƙwararrun malamai	5
6.	Haƙƙokin samar da tsarin koyarwar da ya dace (manhaja)	3
7.	Haƙƙokin sanin 'yancin kai	2
8.	Haƙƙokin a dama da mutum a wajen ɗaukar mataki	3
9.	Haƙƙokin samar da makarantu ingantattu marasa ƙunbiya-ƙunbiya	2
10.	Haƙƙokin samar da ingantacciyar koyarwa	2

Jadawali na sama ya nuna cewa jama'a basa shiga a dama da su a wajen ɗaukar mataki kan wani abu da ya shafi al'umma. Haka kuma ga isassun kayayyakin more rayuwa, amma kuma an tauye musuhaƙƙin samar musu da ingantacciyar koyarwa.

JUYAWAR YANAYI

Garin 'Yammedinada yanayi iri biyu, rani da damina. Ana samun damina yawanci tsakanin watannin Afrilu da Satumba, shi kuma lokacin ranin na zuwa ne tsakanin watannin Oktoba da Maris. Jama'ar wannan gari na samun ruwan da suke amfani dashi yau da kullum mafi kusa ta fanfon tuƙa-tuƙa da kuma rijiyoyi a cikin garin.

Jadawalin da ke tafe zai taimaka mana mu fahimmaci ayyukan da aka fi yi tsahon shekara a wannan gari.



Karin haske: VHSama da Gaske H Sama M Matsakaici L Kasa VL Kasa Sosai

Jama'ar Garin Wajen Samar Da Kundin Cigaban Gari

Matan Garin Wajen Samar Da Kundin Cigaban Garin

Jama'ar Garin Wajen Samar Da Kalandar Yanayin Garin

KADARORI

Ɗaukacin magidanta a garin nada gona ko ƙananan sana'o'i. Mazan garin sunfi yin ayyukan noma akan yan uwansu mata, sai Dai babu wani takamemen ƙiyasi akan adadin maza ko mata akan abin da ya shafi kasuwanci a garin, amma tattaunawar da akayi da mambobin samar da kundin ya nuna cewa maza sun fi yan uwansu mata sana'o'i da kasuwanci. Du ɗan garin na iya mallakar gona ko kiwon shanu ko sauran ƙananan sana'o'i kamar yan tireda, yin man girki. Haka kuma, matan garin nayin sana'ar sayarda Daddawa da sauran kayan miya.

TANTANCE MATSALOLIN DAKE ADDABAR GARIN

Al'ummar wannan garin su bayyana waɗannan matsalolin a matsayin matsalolin da suke addabarsu. Matsalolin su ne:

I. Hanyoyin da suka haɗa garin: lokacin mamakon ruwa ƙananan motoci basa iya shiga garin saboda rashin kyan hanya
II. Saboda rashin gada kan hanyar ruwan Guzuguzu, garin yakan rabe da sauran yankunan garin, ayyukan kasuwanci kan sami tsaiko da komabaya a wannan lokacin, yara basa iya zuwa makaranta sannan marasa lafiya basa iya zuwa asibiti wanda hakan yake barazana ga marasa lafiyar da mata masu juna biyu.
III. Sai kuma matsalar ambaliyar ruwa saboda mamakon ruwan sama da ake samu da kuma yanayin garin.

TANTANCE HAKKOKIN MATA

'Yancin mata shi ne haƙƙoƙinda aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a ƙasashen duniya masu yawa.A wasu wuraren, ire-iren waɗannan haƙƙoƙinana tabbatar da su ne ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar al'umma. A wasu wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a takaita su ga 'yancin yin zabe ko takaita haihuwa ba kaɗai ba.

A arewacin Najeriya, inda garin 'Yammedi yake al'ada da addini suna cigaba da taka muhimmiyar rawa a sha'anin 'yancin mata. An samu cigaba sosai a 'yancin mata musamman wajen faɗaɗa tattalin arziƙinsu da samun damar yin ilimi da kuma yadda suke shiga a dama da su a al'amuran al'umma. Duk da wannan cigaban da aka samu, har yanzu akwai ƙalubale wajen sanya su cikin al'amuran shugabancin da jin ta bakinsu a yayin ɗaukar wata matsaya kan wani al'amari da ba su mukamai da kuma ba su damar bayar da irin tasu gudummawar a sha'anin al'umma.

A garin 'Yammedi, ba a taƙaice damar samun 'yancin ilimin mata ba, watau ana karfafa musu gwiwa su shiga makaranta. Har yanzu akwai adadi mai yawa na matan da aka cire ko sukabar makaranta a dalilin za a yi musu auren wuri da sauran dalilai na gazawar iyaye wajen daukar nauyin karatun nasu da makamanta haka. An yi amfani tsarin cobweb domin a nitsa sosai wajen tantance haƙƙoƙinmata. Aikin yana so ya auna yanayin zamantakewa da tattalin arziƙi da kuma siyasa domin a gano abubuwan da ke kawo tarnaƙi ga cigaban mata a garin.



Hoto5 Ma'aunin Cobweb Na Tantance Hakkin Maza



Hoto6 Ma'aunin Cobweb Na Tantance Hakkin Mata

JADAWALI AYYUKAN YAU DA KULLUN NA GARIN 'YAMMEDI

Anyi amfani da jadawalin ayyukan yau da kullum domin tantance haƙƙoƙin mata a garin domin sanin nauyaye-nauyayen da ke kansu a cikin al'umma. Rukunin mutane daban-daban ne (maza/mata, samari da yan mata) sukayi tantancewar a cikin garin don sanin yadda suke tafiyar da lokutansua ayyuka daban-daban.Jadawalin dake biye ya nuna cewa maza sunfi mata yawan ayyuka haka ma yara maza sun fi yan uwansu yanmata yawan ayyukan yi a cikin al'umma. Yara mazan kan tafi da shanu wajen kiwo, yawanci dukkan ayyukan dake buƙatar amfani da ƙarfi yara mazan ne keyi.



Jadawalin Ayyukan Yau Da Kullun



Duba da rijistar haƙƙin Ɗan Adam, (Anyi amfani da rijistar haƙƙin ɗan adam wajen tantance haƙƙoƙin ɗan adam a cikin al'umma) an gano cewa ana takewa mutanen garin 'Yammedi waɗannan haƙƙoƙin:

- Haƙƙin Samun Abubuwan more Rayuwa
- Haƙƙin Samun Kayayyakin Aiki
- Haƙƙin Samun Ingantaccen Ilimi
- Haƙƙin Samun Abinci
- Haƙƙin ingantacciyar lafiya
- Haƙƙin Samun ingantacciyarRayuwa

Waɗannan haƙƙoƙi nada alaƙa da matsalolin da suke damun wannan garin. Dangane da waɗannan matsalolin da ake takewa, al'ummar wannan garin sun yanke cewa ana take musu haƙƙoƙin ababan more rayuwa kamarsu wutar lantarki, hanyoyin mota da hanyoyin sadarwa na wayar salula.Daɗin daɗawa kuma an tauye musu haƙƙin ingantattun ababan more lafiya a garin.

Lissafin Haƙƙoƙin Garin 'Yammedi

Jihar /LRP	KANO			KARAMAR HUKUMA	KARAYE		GARI		KADEMI	
Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano)	Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da aka yi shirin		Al'amari	Abubuwan da suka haddasa	Haƙƙoƙin da aka tauye	Kundin tsarin mulki	Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin		Waɗanda nauyin yin aikin ya hau kansu	Sauran muhimman masu ruwa da tsaki
	Namiji	Mata					Namiji	Mata		
Maza, Mata, Matasa da Yara	12,644	10,631	Rashin Kyakkyawar Hanyar mota da gadoji	Matsalar kuɗi.	Haƙƙin samun ingantattun ababan more rayuwa	Kundin Tsarin Mulkin ƙasa	12,644	10,631	Majalisar ƙaramar hukuma. Kansilan ayyuka. Ma'aikatar ayyuka ta Jiha Maaikatar ayyuka ta tarayya	Kamfanonin gine-gine.
Maza, Mata, Matasa da Yara	12,644	10,631	Karancin tsaftaceccen ruwan sha	Rashawa da cin hanci a matakai daban-daban.	Haƙƙin samun ingantacciyar lafiya da kayayyakin aiki	Kundin Tsarin Mulkin ƙasa	12,644	10,631	Ma'aikatar ruwan sha t a jiha.	Kungiyoyi masu zaman kansu Sassan majalisar ɗinkin duniya
Maza, Mata, Matasa da Yara	12,644	10,631	Karancin kayayyakin lafiya da ma'aikatan lafiya	Rashin ƙaddamar da ayyuka	Haƙƙin samun ingantacciyar lafiya.	Kundin Tsarin Mulkin ƙasa	12,644	10,631	PHMB. Ma'aikatar lafiya ta jiha	Kungiyoyi masu zaman kansu Sassan majalisar ɗinkin duniya
Maza, Mata, Matasa da Yara	12,644	10,631	Ilimi: ƙarancin kayayyakin koyo da koyarwa da ƙarancin malamai	Rashin ƙaddamar da ayyuka	Haƙƙin Samun Ingantaccen Ilimi .	Kundin Tsarin Mulkin ƙasa	12,644	10,631	Ma'aikatar ilimin firamare da bai ɗaya.	Kungiyoyi masu zaman kansu Sassan majalisar ɗinkin duniya
Maza, Mata, Matasa da Yara	12,644	10,631	Noma (noman rani)	Rashin amfani da damarmakin da ake dasu (shirin noman rani)	Haƙƙin Samun Kayayyakin Aiki	Kundin Tsarin Mulkin ƙasa	12,644	10,631	Ma'ikatar ilimi ta jiha Ma'aikatar noma ta jiha,	Ma'aikatar noma ta ƙasa
Maza, Mata, Matasa da Yara	12,644	10,631	Rashin aikin yi/ sana'o'i/ mata/masu buƙata ta musamman	Rashin amfani da damarmakin da ake dasu (shirin noman rani)scheme)		Kundin Tsarin Mulkin ƙasa	12,644	10,631	Ma'aikatar yaɗa labarai da cigaban matasa ta jiha	Majalisar ƙaramar hukuma.

CHALLENGE

KALUBALEN DA KE FUSKANTAR GARIN 'YAMMEDI A HALIN YANZU



KALUBALEN **DA KE FUSKANTAR GARIN 'YAMMEDI A HALIN YANZU**

Kalubalen dake fuskatar garin 'Yammedi a halin yanzu sun haɗa da rashin ababan more rayuwa kamar wutar lantarki, ilimi, asibiti da sauran kayayyakin da suke taimakawa al'umma wajen cigabansu. Makarantar firamaren ƙwalli ɗaya da ake da itanada ƙarancin ajujuwa da ƙwararrun malamai, yanayin da ilimi ke ciki a wannan gari shi ke bada ƙarin haske kan yanayi da harkokin lafiya ke ciki a garin. Wannan gari nafuskantar yawan matsalar mutuwar mata masu juna biyu da ƙananan yara saboda matsalolin da ke akwai a harkokin da suka shafi lafiya. Yanayin da hanyoyin garin ke ciki yayi mutuƙar taka rawa wajen kawo tangarɗa a harkokin lafiya kuma yana buƙatar duba na tsanaki wajen shawo kan matsalolin lafiyar garin.

A lokutan damuna, rayuwa kanyi mutuƙar wahala a wannan gari, ba ko yaushe yara ke zuwa makaranta ba, marasa lafiya basa iya zuwa asibiti haka nan jama'a ba sa iya ɗaukan kayayyaki zuwa kasuwa saboda rashin kyan hanya da matsalar zaizayar ƙasa musamman hanyar Rogo/Karaye zuwa Tofa wadda ta wuce cikin garin 'Yammedi zuwa Kabo, Rimin-Gado da Tofa.

Akwai hanyar ruwa (Kogi) a 'Yammediwadda kebayar da gudunmowa ƙorai da gaske wajen noman rani. Idan aka sake ginata za a ci moriyarta wajen noman rani. Wannan zai rage matsalar rashin aikin yi da jama'ar wannan gari ke fuskanta. Haka kuma zai rage matsalolin yau da kullun ya kuma bunƙasa yanayin rayuwa a wannan gari.

Masu Buƙata ta musamman basa cin moriyar duk abubuwan da suka shafi ilim hakan kan yi musu barazanar samun kyakkyawar rayuwa a gaba.

An jera matsalolin wannan garin ta hanyar tsarin na matsalar da tafi ciwa al'umma tuwo a ƙwarya a sama (duba jadawalin dake tafe), jama'ar garin sun saka matsalar

Hanya da Ggadoji matsayin matsalar da ake bukatar a fara magantawa. Al'ummar wannan gari suna da kyakykyawan zato cewa samar da hanya zai haɓaka rayuwarsu kamar yadda matsalar da ta shafi lafiya (ƙarancin kayayyakin lafiya da ma'aikatan lafiya) ta zama matsala ta huɗu da ke mutukar tauye cigaban rayuwarsu.Rashin aikin yi musamman a gurin matasa, mata da masu buƙata ta musamman itace matsala ta biyu de ke ci musu tuwo a ƙwarya, matsalar ruwan sha tazo ta uku. Ilimi na ɗaya daga cikin abubuwan da suke fuskantar matsaloli a garin. Al'umar wannan gari nada ra'ayin cewa samar da babbar makaranta ta gaba da sikandire a yammacin Kano zai taimaka wajen jawo ra'ayin mutanen yankin su cigaba da karatu a yankin.

SASSAUKAR **HANYAR JERA MATSALOLI**

Domin faɗaɗa tantance matsalolin anyi amfani da sassaukar hanyar jeran matsaloli don samun matsaya kan yadda za a magance su.

YAMMEDI COMMUNITY — PAIR WISE RANKING

	ISSUES	WOMEN	CHILDREN	MEN	TOTAL	RANK
1	Road-karaye-Kano	= 25	35	54	214	1st
2	Health	= 12	5	32	49	4th
3	portable water	= 03	10	47	60	3rd
4	Education	= 13	10	18	41	5th
5	Erosion	= 02	3	18	23	6th
6	Agriculture Fertilizers & farm tools	= 00	2	16	18	8th
7	Empowerment (women, youth & PWD)	= 42	20	17	79	2nd
8	Electricity	= 04	5	10	19	7th

SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI

AL'AMARI	MATA	YARA	MAZA	ADADI	MATSAYI
Hanya Babbar hanyar da ratsa LG 5 daga rogo zuwa Tofa	25	35	154	214	214
Lafiya	12	5	32	4	4
Ruwan Sha	3	10	4	60	60
Ilimi	13	10	18	41	41
Zai zayar Kasa	2	3	18	23	23
Noma (taki da sauran kayan aikin gona)	0	2	16	18	18
Rashin aikin yi/ Dogaro da kai/ Mata da Masu Bukata ta musamman (PDWs)	42	20	17	79	79
Wutar Lantarki	4	5	10	19	19

Gudanar Da Zaɓe

Gudanar Da Kidaya

TANTANCE MATSALOLI TA AMFANI DA BISHIYAR MATSALOLI



Ita wannan bishiya na taimakawa wajen faiyace matsalolin al`umma da aka binchiko.Ita wannan bishiya tana nuna dangantakar waɗannan matsaloli da dalilan afkuwarsu da kuma illar da suke da ita idan ba a magance su ba. Don haka, kai tsaye za a tafi kan tushen matsalar domin magance matsalar gabaɗaya. Tushen matsalar jama'ar wannan gari shi ne rashin hanya ganyan bishiyar kuma shi yake nuni da abin da matsalar zata jawo idan ba a magantata ba. Ga dai yadda bishiyar matsalolin take.

Tushen matsalar Hanyar wannan gari shi ne matsalar jagoranci nagari, rashin kuɗi, ƙarancin ilimi, ƙarancin ƙungiyoyin sakai, ƙarancin ma'aikatan gwannati da kuma ƙarancin fitattun yan book da yan kasuwa.

An bayyana dalilan da suka jawo waɗannan matsalolin kamar haka: ƙarancin himmar aiki, taɓarɓarewar tattalin arziƙi, yawaitar yaɗuwar zaman banza, wahalhalun rayuwa, ƙaruwar mutuwar mata masu juna biyu, ɓarkewar cututtuka saboda rashi kawo agajin gaggawa da wuri, da rashin cigaban gari.

Dangani da waɗannan lammuran da suka taso daga bishiyar matsaloli a wannan gari, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar 'Yammedi sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a garin.

JADAWALIN TANTANCE MATSALOLI GARIN 'YAMMEDI

ABUBUWAN DA AKA GANO	WAƊANDA ZA SU IYA TALLAFAWA	CIBIYOYI	MANYAN BUKATU/ ZABURARWA DOMIN KAWO CANJI	MATAKIN KARFIN IKON KAWO CANJI (SAMA TSAKA-TSAKI KO NA-KASA)
Hanya da Gadoji	1. Kansila 2. Shugaban Karamar Hukuma 3. Ɗan majalisar jiha 4. Ɗan majalisar tarayya 5. Gwamnan Jihar Kano 6. Kwamishinan ayyuka da gidaje 7. Kwamishinan ƙananan hukumomi 8. Shugaban sashin ayyuka na ƙaramar hukumar Karaye	Sashin ayyuka na ƙaramar hukuma Kwamitin ayyuka na majalisar jiha. Gwamnatin jihar Kano Ma'aikatar ayyuka Ma'aikatar ƙananan hukumomi.	Cigaba Siyasa Siyasa Siyasa Siyasa Siyasa Siyasa Cigaba	 1.L 2.H 3.M 4.M 5.H 6.H 7.M 8.M
Ruwan Sha	1. Kansila 2. Mai Unguwa/Dagaci 3. (Shugaban sashin lafiya) 4. Shugaban Karamar Hukumar Karaye 5. Ɗan majalisar jiha 6. Ɗan majalisar tarayya Sanata 7. Kwamishinan ƙananan hukumomi 8. Daraktan hukumar lafiya	Sashin Lafiya na ƙaramar hukuma Ma'aikatar lafiya ta Jihar Kano W.H.O UNICEF Hukumar Lafiya ta Jiha Kwamitin Lafiya na Majalisar Jiha.	Siyasa Cigaba Cigaba Cigaba Siyasa Siyasa Siyasa Cigaba	1.L 2.L 3.M 4.H 5.H 6.M 7.M 8.H
Ilimi: Karancin Ajujuwa, Malamai, damakarantar gaba da sikandire ga matasa	1. Sakataran Ilimi na ƙaramar hukumar ƙaraye 2. Kansila 3. Kwamishinan Ilimi 4. Darakta, Maikatar Ilimin firamare na bai ɗaya	Kwamitin Ilimi na ƙaramar hukumar Karaye Kwamitin Ilimi na Jiha. Ma'aikatar Ilimi (SUBEB, KSSSMB)	Siyasa Siyasa Siyasa Cigaba	1.M 2.L 3.H 4.H

TANTANCE YANAYIN KARFIN IKO (NAZARI KAN WAƊANDA KEDA IKO)

An yi amfani da tsarin zane naVenn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma shi wannan ma`auni an yi amfani da tsarin zanen Venn domin tantance matakin ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi ke da shi da kuma alaƙarsu da juna.Zanen dake tafe ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano. Sanan kuma zanen ya nuna tazarar da mutane da cibiyoyin suke daga garin da kuma alakar su da juna



Ƙarin Bayani:

Zanen dake tafe ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano. Sanan kuma zanen ya nuna tazarar da mutane da cibiyoyin suke daga garin da kuma alaƙar su da juna

Jama'ar Yammedi sun nuna cewa gwamna da gwamnatin jihar kano tana da tasiri wajen samar da wannan babbar hanya, wacce zata ƙara haɓaka kasuwancin yankin dama jiha baki daya. Kwamitin Majalisa akan ayyuka da gidaje yana da tasiri wajen kawo gyara wajen gina hanya Rogo zuwa Tofa da ma'aikatan ayyuka da ginegine. Kwamitin ayyuka a majalisar jiha na da ruwa da tsaki wajen samar da hanyar kuma yana da tasirin maganta wadannan lammuran. Sanan kuma majalisar ƙaramar hukuma itama nada rawar takawa wajen sa lamarin gaba. Alaƙarta da ma'aikatar ƙananan hukumomi da ƙaramar hukuma kan sa a maida hankali wajen magance matsalolin.

Alaƙar da ake da ita tsakanin masu sarautun gargajiya, malaman addini da masu aikin gwamnati zasuyi mutuƙar taimakawa wajen magance wannan matsalar.

TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Garin 'Yammedina samaun bayanai daga waje ta hanyar zantuttukan al'umma, Jaridu, Radiyo, Talabijin, masu shela, wayar tafi da gidan ka, Yanar gizo (wato hanyoyin sadar wan a zamani Facebook da Twitter)

Haka kuma suna musayar bayanai da mutane da cibiyoyi ta hanyar wasiƙa da kuma saƙunan baka.



TSARIN DA AKA SHIRYA GUDANARWA NA AL`UMAR GARIN 'YAMMEDI

A ƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran tsarin da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar yinamfani da gudummawar kowa da kowa da wasu dabaru domin tantance abubuwan da ke ci wa al'ummar garin

MAHIMMAN BATUTUWA	AIKIN DA AKA TSARA GUDANARWA	WAƊANDA SUKA ƊAUKI NAUYI	KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA	KAYAN AIKIN DA AKE BUKATA	MATSALOLI	SHAIDAR SAMUN NASARA
Rangadi don saduwa da sauran jama`ar garin 'Yammedi	Ganawar baka da baka	Kwamitin samar da kundin Cigaban 'Yammedi	Sati 2 zuwa 20 ga watan Satumba	Bayani game da wannan shiri	Kudi	Rahoto Daftarin cigaban unguwa
Daftarin cigaban gari	Gabatarwa da amsar bayanai	CITAD/ jama'ar garin	Sati 3 zuwa 27 ga watan Satumba	Daftarin cigaban gari	Zirga zirga	Ranar ƙaddamarwa
Kaddamawar	Raba wasiƙun gaiyata	CITAD/ jama'ar Garin		Daftarin cigaban unguwa na karshe Raba wasiƙun gaiyata	Ganawa akan jujjuyarwar yanayin Shekara (Damuna)	Kaiwa da komowa rahoto
Rangadi don saduwa da sauran jama`a	Ziyarar gaisuwa da rokon iri	CITAD/ jami`in unguwa	30 ga watan Nuwamba 2015.	Kwafin Daftarin cigaban garin	Ayyukan noma.	